GUDUNMAWAR MATA MASU ADDINI

GABATARWA: Mata iyaye ne ga al'umma kuma mataimaka ne ga addini idan suka fahimci addinin. A rayuwar yaro babu wani mai tasiri (tun daga farko har 'karshen ta) kamar mahaifiyar shi. Uwa makaranta ce ta farko kuma duk wani karatu bayan nata zai zo kuma 'kar'kashin shi zai kasance. Gudunmawar da mata suka bawa musulunci yasa babu ranar da tarihin cigaban musulunci zai manta da gwagwarmayar da suka yi. Na rubuta wannan littafin mai suna GUDUNMAWAR MATA MASU ADDINI don kawo wani 6angare na gwagwarmayar da mata suka yi musamman wajen karantar da 'ya'yan su addini da kuma taimakawa addini da suka yi a rayuwar su da kuma tasirin haka don su zama ababen koyi ga mata musulmai.

© ANSARULLAH

+2348067396502

(1)

A lokacin mulkin bani Umayyah (bayan mulkin khalifofin Manzon ALLAH SAW) lokacin musulunci ya fad'ad'a a gabashin duniya, a lokacin ne aka d'aura auren wani matashi mai suna Farukh da matar shi mai suna Suhaila. Taron auren ya samu halartar wasu sahabbai da tabi'a a birnin madinar Manzon ALLAH. Angon da amaryar masu addini ne wanda hakan ne yasa suka yi fice har tarihin su yayi shura a gurin manyan malamai bayan zamanin su. A wancan lokacin, jihadi na fita fagen daga don d'aga kalmar ALLAH yana cikin ayyuka mafiya falala da ko wane musulmi yake kwad'ayi kuma yake mafarkin yi. A lokacin musulmai suna zagayawa ko wane yankin duniya don isar da musulunci. Wannan matashin (Farukh) wanda yayi sabon aure, yana kusantar sahabbai da sauran tabi'ai masu zuwa jihadi kuma yana jin nasarorin da suke samu wajen isar da musulunci da kuma yadda suka bada rayuwar su wajen d'aga kalmar ALLAH. Ba'a kai watanni uku da auren ba wata rana ya dawo gida da daddare ya gayawa matar shi niyyar shi ta tafiya jihadi. Duk da ba'a kai watanni uku da auren ba, samun yardar ALLAH shine ya zamanto mafi soyuwar aiki a gurin sa kuma yafi kwad'ayin zuwa jihadi sama da zama tare da matar shi. Abu ne mara yiwuwa kuma ba wanda za'a yarda dashi ba a gurin matar tashi saboda yaushe yaushe aka yi auren da har zai tafi ya barta? Idan ya tafi wa zai kula da ita? Yaushe za ta iya zama a gida ita kad'ai? Wa zai taya ta zama a gidan a 'karancin shekarun ta da ya aure ta ya raba ta da gidan iyayen ta? Ta tambaye shi abubuwa da yawa amma amsa d'aya ya bata da yace: "ALLAH zai kula dake". Tunda ya yanke shawarar tafiya jihadi bashi da lokacin 6atawa saboda haka sai kawai ya hau shirin tafiya kuma a daren yayi ta rarrashin matar tasa yana 'ko'karin nuna mata cewa wannan dama ce da ya samu kuma bai kamata yayi wasa da ita ba kuma zai yi jihadin ne don neman yardar ALLAH. Ya tafi ya bar mata wasu 'kud'ad'e wad'anda

za ta yi amfani dasu na 'yan watannin da zai yi baya nan kuma ya bar mata dinari dubu talatin a matsayin ajiya wanda yace kar ta ta6a har sai ya dawo. Haka suka rabu tana kuka tana cewa: "Farukh kar ka tafi ka bar ni. Idan ka tafi wa zai kula dani?" Bai ce mata komai ba sai cewa ALLAH zai kula dake. Farukh ya tafi masallacin Annabi yayi sallar Asuba a masallacin sannan suka yi ayari suka wuce tare da sauran wad'anda zasu tafi jihadin tare. Suhaila ta d'auki lokaci tana kuka bayan ya tafi har 'kawayen ta suka zo suka ta rarrashin ta suna ta 'ko'karin kwantar mata da hankali amma ta kasa ha'kura. A haka rayuwa ta cigaba da tafiya kuma ba'a kai watanni uku ba bayan tafiyar mijin nata ta gano ashe ta samu ciki. Ashe tana da cikin Farukh a jikin ta kafin ya tafi, bai sani ba ita ma bata sani ba. Tana 'kara shiga 'kunci matu'ka a duk lokacin da ta tuno cewa za ta haifi yaro kuma ya tashi a matsayin maraya (saboda har lokacin mijin nata bai dawo ba) amma ba ta da wani za6i sai na ro'kon ALLAH ya bata mafita. A kwana a tashi aka wayi gari ta haifi d'a namiji, ta ji dad'in haifar yaron amma bata san yadda zai rayu ba tare da uba ba. Tana yawan tambayar musulman da suka dawo daga jihadi akan mijin ta amma babu wanda ya ta6a bata wani bayani gamshashshe a kan shi. Kud'in da ya bar mata sun kusa 'karewa gashi bata da niyyar ta6a komai daga ajiyar da ya bata. Haka ta yi ta ha'kuri har wata rana taji wasu gungun mujahidai sun dawo madina, a lokacin ta tafi gurin su tana fatan samun bayani akan mijin ta. Da ta tambaya sai wani daga cikin su yace mata: "Na gan shi da ido na yana gargarar mutuwa a d'aya daga cikin ya'ku'kuwan da aka yi". Abinda kunnen ta ya jiye mata akan mijin nata ba mai sau'kin ji bane a gare ta amma saboda imanin da yake zuciyar ta ba ta iya yin wani mummunan abu ba sai cewa: " INNA LILLAHI WA INNA ILAHHIRRAJI'UN". Bayan ta tafi gida cikin damuwa haka ta kasance cikin tsananin kunci har sai da ga bata da mafita sai ta mi'kewa ALLAH lamarin ta. Bayan wannan labarin da ta samu na mutuwar mijin nata sai ta fara amfani da dukiyar da mijin nata ya bata ajiya wajen bawa d'an da ta haifa ilimin addini. Tana dau'kan shi tana kai shi manyan majalisun malaman madina kuma tana d'auko malamai gida suna karantar dashi Qur'ani da hadisan manzon ALLAH. Tana dau'kan nauyin karatun ne da abinda mijin nata ya bata ajiya kafin ya tafi jihadin da aka ce mata ya mutu a can. Malaman da suke karantar da d'an nata sun lura da baiwa da haza'kar da ALLAH ya bawa yaron. 'Ko'karin da yaron yake dashi wajen karatu da haza'kar sa sun taimaka masa ba wajen amma abinda yafi taimaka mai shine fad'i tashin da mahaifiyar shi ta dinga yi akan karatun nasa da addu'o'in da take mishi da sa masa albarka. Shekaru suna tafiya amma har lokacin Suhaila bata daina tunanin mijin ta ba, tana fatan ganin shi wata rana. Tana bawa d'an nata labarin shi kuma tana koyar dashi kyawawan halaye da d'abi'un mahaifin nasa.

Wani dare bayan shekaru talatin a iyakar 'kasar Sin (China) guri mai matu'kar nisa daga madinar Annabi, muhajidai suna barci bayan ALLAH ya basu nasara a wani ya'ki sun kwanta da farin ciki kuma barcin nasu yayi tsawo sakamakon gajiyar da suka yi. Kowa yana kwance yana barci banda wani tsoho wanda daga ganin shi ya wuce shekaru hamsin. Wannan tsohon abinda ya hana shi barci shine tunanin matar shi da ya baro ta tun basu wuce watanni uku da aure ba. Lokacin da kowa yake

barci, shi kuma wannan tsohon yana cewa: "Me ya faru da Suhaila? Ya take? Me ya faru da da amanar da na bata??" Tambayoyi da dama sun zo zuciyar sa a wannan daren wanda hakan yasa ya yanke shawarar komawa madina don ganin matar shi kafin ALLAH ya d'auki ran d'aya daga cikin su. Ya nemi izinin jagoran su kuma ya d'auki hanyar komawa madina duk da tsawon tafiyar da take gaban shi. Duk da nisan da tafiyar take dashi, son ganin matar shi da son sanin halin ta take ciki su suka 'kar'kafa shi akan tafiyar. Haka ya cigaba da tafiya kuma a duk lokacin da yake 'kara kusa da madina, lokacin ne damuwar shi take 'kara yawa yana tambayar kan sa shin ko a wane hali zai samu matar sa?

Bayan tafiyar tsawon watanni, daga 'karshe ya isa madina garin da ya bar matar sa sama da shekaru talatin da suka wuce. Duk da tsananin 'kaguwar da yayi na ganin matar shi hakan bai hana shi tunawa da sunnar Annabi (SAW) ta fara shiga masallaci tare da yin nafila raka'o'i biyu bayan ya dawo daga tafiya kafin ya wuce gida ba. Bayan Farukh ya shiga masallacin Manzon ALLAH yayi nafila raka'a biyu lokacin sallar la'asar ya kusa saboda haka sai ya jira aka yi sallah, bayan an yi sallar la'asar d'in sai yaga mutane masu yawa sun zazzauna sun zagaye wani mutum matashin malami. Yayi mamakin wannan majalisin saboda a kaf rayuwar da yayi a madina bai ta6a ganin irin majalisin wannan malamin ba. Yadda yake tafiyar da d'aliban sa da salon karantarwar sa sun burge shi matu'ka. Daga cikin d'aliban wannan babban malamin akwai Imam Malik d'an Anas (d'aya daga cikin malaman mazhabobi hud'u da suka cika duniya da ilimi) da kuma fitaccen malamin nan mai suna Sufyanuth-Thauri da Imam Laith bin Sa'ad da sauran mashahuran malamai na wancan lokacin. Farukh ya tambayi wani mutum wanda yake zaune a kusa dashi yace: "Wane malami ne wannan?" Sai mutumin yayi masa dariya yace: "Kana nufin baka san wannan fitaccen malamin ba?" Sai Farukh ya bashi amsa da cewa: "Ni ba'ko ne ba a nahiyar nan nake ba". Sai mutumin yace masa: "Sunan shi Rabi'a bin Abdurrahman". Farukh bai iya ganin fuskar shi ba saboda yana da nisa dashi kuma d'alibai sun kawaye shi. Bayan an kammala karatun mutane suna fita daga masallacin don komawa harkokin su sai shima Farukh ya fito daga masallacin ya nufi tsohon gidan shi. Ya gane gidan amma sai yaga wani mutum cikin shiga ta kamala zai shiga gidan. Farukh ya kasa ha'kuri ganin wani zai shigar mishi gida ba tare da izinin shi ba saboda haka sai ya nufe shi don dakatar dashi. Ya ri'ko shi yace: "Kai waye? Me zaka shiga yi a gida na? Wa ya baka izinin shiga min gida??" Wannan mutumin yayi 'ko'karin kare kan shi a dai dai lokacin da shima yake yiwa Farukh irin tambayoyin da ya mishi. Da suka fara hayaniya sai mutane suka fara taruwa kuma daga cikin mutanen da suka zo akwai imam Malik har ma ya cewa Farukh: "Bamu san ka a nan ba, wannan ba gidan ka bane (na wannan malamin ne ya nuna mutumin da suke jayayya da Farukh)". Da Farukh yaji mutane suna cewa gidan mutumin ne ba nashi ba, sai yace: "Ni ne Abdurrahman Farukh, gidan nan nawa ne". Ko mintina biyu ba'a 'kara ba sai wata mata tsohuwa ta fito daga cikin gidan tace: "Farukh ne! miji na ne!!" Sai kuma ta kalle shi tace: "Wannan d'an ka ne, ka sake shi!". Mutanen da suke gurin sai da suka yi hawaye saboda al'amarin sai kuma kowa ya watse. Farukh da matar shi Suhaila suka shiga gida, shi kuma d'an

nasu (wannan malamin) sai ya fita ya bar su. Farkon abinda Suhaila ta fad'awa mijin nata da suka shiga gida bayan rabuwar tsawon shekaru shine: "Kayi ha'kuri Farukh, yanzu bani da kyau kamar yadda ka sanni shekaru sama da talatin da suka wuce saboda tsufa. Gashin kai na ya zama fari, fata ta kuma ta yamutse". Sai Farukh yace mata: "Ban damu da wad'annan abubuwan ba. Kyawun ki yana zuciyar ki. Kyawun ki shine gaskiyar ki da halayen ki da d'abi'un ki". Haka wad'annan masoyan suka ta hirar yaushe yamo har ya tambaye ta akan amanar da ya bata (na dinari dubu talatin wanda ya bata ajiye kafin ya tafi shekaru sama da talatin da suka wuce). Tace: "Ba kace min da ka dawo ka shiga masallacin Annabi kafin ka zo nan ba?" Yace: "Eh haka ne". Tace: "Me ka gani a masallacin?" Yace: "Naga wani malami mai abun mamaki wanda ban ta6a ganin irin shi ba kuma ba zan ta6a mantawa dashi a rayuwa ta ba". Suhaila tace: "Zaka so zama malami kamar shi ko da zaka bada duka dukiyar da ka bani ajiya?" Sai Farukh yace: "Zan so zama kamar shi ko da zan rasa duk abinda na mallaka". Sai ta 'kara tambayar shi: "Zaka so ka kashe duka dukiyar da ka bani ajiya don ka samu d'a (yaro) irin wannan malamin?" Ya amsa da cewa: "Zan so in samu d'a kamar shi ko zan mallaki komai na duniya kuma in bada shi don d'a na ya zama kamar shi". Suhaila tace: "To Rabi'a bin Abdurrahman d'an ka ne kuma dashi ne kuka yi jayayya d'azu a rashin sani". Da jin haka sai Farukh ya tashi yana zagayawa yana cewa: "Ta yaya Rabi'a d'an Abdurrahman zai zama d'a na? Da ta bashi labari sai yayi ta mamaki yana cewa: Yanzu dama ashe Rabi'a bin Abdurrahman Farukh d'a na ne?! Ya cigaba da cewa: "ALLAH ina matu'kar godiya a gare ka bisa wannan kyautar da ka min"

(2)

Wani bawan ALLAH mai suna Abu Qudama Ash Shamy (mutumin Sham) wanda ya zauna a Madina yayi fice akan jihadin don d'aga kalmar ALLAH. Wata rana shi da abokan sa suna tattaunawa a masallacin Manzon ALLAH (SAW) sai suka ce masa: "Abu Qudama ka bamu labarin abinda yafi baka mamaki a rayuwar jihadin ka". Sai yace: Wata rana na isa birnin Riqqa (na Iraq) don siyan ra'kumin da zai d'aukar min makamai (kayan da na siya). Wata mata ta shigo inda nake zaune sai tace: "Ya kai Abu Qudama! Naji yadda kake son yin jihadin da 'ko'karin ka na janyo musulmai don suyi jihadi. ALLAH ya albarkace ni da yawan gashi sama da mata da yawa don haka na yanke shi kuma had'a linzamin doki dashi kuma na rufe shi da toka saboda kar a gane. Zan so ka dau'ke shi ka tafi dashi, idan ka tafi dashi har garin mushrikai kuma aka fara ya'ki, zaka iya amfani dashi ko ka bawa wani yayi amfani dashi. Ni dai kawai abinda nake so shine gashi na yaje ya'ki kuma yayi 'kura a fagen d'aga kalmar ALLAH. Ni bazawara ce wacce take da miji da dangi wad'anda aka kashe su a fagen d'aga kalmar ALLAH. Idan akwai bu'katar nima in yi jihadi, zan shiga ayi dani nima. (Ta cigaba da cewa) Miji na mutu ya bar min yaro wanda yana cikin mafiya kyawun samari, ya koyi Qur'ani da salon ya'ki da kuma harbi. Yana yawan sallar dare kuma yana yawan yin azumi da rana, shekarun sa sha biyar. Ya tafi kula da abinda ya gada daga baban shi. Ina kyautata zaton zai dawo kafin ku tafi don ina

son in yi kyauta dashi zuwa ga ALLAH mabuwayi madau'kaki. Ina ro'kon ka don ALLAH kar ka hana ni samun ladan da nake nema." Abu Qudama yace: Bayan mun kama hanyar fita daga Riqqa sai muka ji sautin wani daga can bayan mu yana cewa: "Ka jira ni ya kai Abu Qudama! ALLAH ya gafarta maka. Na tsaya na umarci wad'anda muke tare dasu akan suje su ga ko waye. Wanda yake kan dokin sai ya 'karaso inda nake ya rungume ni yace: Godiya ta tabbata ga ALLAH wanda bai haramta min kasancewa da kai ba kuma bai mayar dani gida ba ina ba'kin ciki. Nace: Yaro bari in ga fuskar ka da kyau don naga ko ka cancanci zuwa ya'ki, idan baka cancanta ba in mayar da kai gida. Da na bud'e fuskar shi sai na ga kyakkyawan matashi kamar hasken wata (don kyau) kuma yayi kama da wanda yake rayuwa cikin wadata da jin dad'i. Nace: Kana da mahaifi (a raye)? Yace: A'a, sai dai ma nazo ne don in d'auki fansa akan kisan da aka yiwa baba na kuma ta yiwu nima ALLAH yasa in samu shahada kamar yadda baba na ya samu. Nace: Shin kana da mahaifiya (mahaifiyar ka tana raye)? Yace: Eh. Nace: To kaje ka tambayi izinin ta, idan ta amince sai kazo mu tafi da kai, idan kuma ba ta amince ba sai ka koma ka zauna a gurin ta. Yace: Abu Qudama baka gane ni ba? Nace: Eh. Yace: Ni ne d'an matar da ta baka linzamin doki. Ya aka yi ka manta da mama na da sauri haka? Ya aka yi ka manta alfarmar mama na da wuri haka? in shaa ALLAHU ni ne shahidi d'an shahidi! Ina ro'kon ka don ALLAH kar ka hana ni tafiya da kai a hanyar ALLAH saboda na haddace Qur'ani kuma ina da ilimin sunnonin Annabi (SAW) kuma na iya sarrafa doki da harbi kuma a inda na baro ban bar wani da ya fini iya ya'ki ba (babu wanda ya fi ni 'kwarewa a sa'anni na) saboda haka kar ka damu da 'karancin shekaru na. Mahaifiya ta tayi bakance akan ba zan koma ba kuma tace min: "Ya kai d'ana! Idan ka gamo da kafirai kar ka juya musu baya (kar ka gudu), ka bada rayuwar ka ga ALLAH, ka nemi kusanci zuwa ga ALLAH kuma zuwa ga baban ka da sauran salihan kawun nan ka a Aljanna kuma idan ALLAH yasa kayi shahada to ka ceci ni (daga wuta zuwa Aljanna) saboda an gaya min cewa shahidai suna ceton yan'uwan su guda saba'in da makwabtan su mutum saba'in". Sai ta rungume ni kuma ta d'aga idanun ta sama tace: "Yaa Mahalicci na, wannan shine yaro na kuma sanyin idanu na kuma mafi soyuwa a zuciya ta. Na sadaukar maka dashi Ka kusantar dashi zuwa ga mahaifin sa"

Lokacin da naji maganganun yaron sai da nayi hawaye domin kyawawan dabi'un sa da kuma tausayawa mahaifiyar sa kuma nayi mamakin ha'kurin da ta za6i yi na rashin shi a kusa da ita. Muka cigaba da tafiya dashi har sai da dare yayi muka yada zango, da asuba tayi kuma muka shirya muka cigaba da tafiya. Tsawon lokacin nan yaron nan bai bar ambaton ALLAH da girmama ALLAH ba. Na lura dashi sosai kuma na fahimci ya fi mu lokacin da muke tafiya kuma shine mai mana hidima lokacin da muka yada zango. Muna 'kara kusantar abokan gaba yana 'kara 'karfafa mu, zuciyar sa tana 'kara tsarkaka kuma farin cikin sa yana 'kara bayyana. Lokacin da muka kusa isa iyakar kafirai dare yayi saboda haka sai muka kafa sansani, yaron nan yana dafa mana abincin bud'a bakin azumin da muke yi sai barci ya d'auke shi. Ya d'au lokaci yana barci kuma ina iya ganin murmushin shi a lokacin da yake barcin. Bayan ya tashi sai nace: 'Dana naga kana ta murmushi a lokacin da kake barci. Yace: "Nayi

mafarki ne shi ya saka ni murmushi" Nace: "Me ka gani?" Yace: "Na ganni a wasu kyawawan korayen kaya masu 'kyal'kyali ina kan mamaki sai naga wata fada wacce aka gina ta da zinari, matattakalun ciki an yi su ne da lu'u lu'u da marjani. 'Kofofin an yi su ne da gwala gwalai kuma labulayen an saukar dasu sai naga kuyangu kyawawa fuskokin su kamar farin wata ta labule. Da suka ganni sai suka ce: Sannu da zuwa. Sai kuma naji wasun su suna gayawa yan'uwan su cewa: Shine mijin mu mai albarka. Sai suka ce min: Ka taho, ALLAH ya maka rahama. Lokacin da na tafi gare su sai naga wani d'aki a saman fadar wanda aka yi shi da jajayen gola golai kuma akwai gado wanda aka yi da korayen lu'u lu'u, 'kasan gadon kuma an yi shi da fararen azurfa. A kan gadon akwai wata mace wacce kamar rana take don haske, ba don taimakon ALLAH ba da na rasa idanu na saboda hasken jikin ta da hasken da yake da'kin. Ta gaishe ni kuma tace: Kai nawa ne kuma nima taka ce. Sai na nufe ta zan rungume ta, da taga abinda nake shirin yi sai ta dakatar dani tace min: Ka dakata tukun, kai baka cikin masu aikata haram. Ka bari sai gobe zamu had'u da kai lokacin sallar Azahar saboda haka kayi farin ciki!".

Abu Qudama yace masa: Babu abinda ka gani sai alkhairi kuma zai tabbata da yardar ALLAH. (Abu Qudama Ya cigaba da bada labari yana cewa) Bayan mun yi barci mun tashi washegari, sai mahaya dawakai daga cikin mu suka hau saman dutse kuma mai kira yayi kira yace: "Ya ku mahaya! Ku haura kuma kuyi farinciki da samun Aljanna (idan kun yi shahada). Ku fita kuna marasa nauyi ko kuna masu nauyi kuma kuyi jihadi da dokiyoyin ku da kawunan ku don d'aga kalmar ALLAH, hakan shine alkhairi a gare ku idan kun sani (Suratut Tauba, aya ta 41)". Ko sa'a d'aya ba'a yi ba sai ga kafirai sun nufo kamar namun dawan da aka koro. Mutum na farko da ya farmake su shine yaron nan, ya watsar dasu, ya kashe da yawa daga cikin su kuma ya kashe gwarazan su. Da naga yadda yaron yake shiga cikin su sai nayi wuf na ri'ke linzamin dokin sa nace masa: Kai yaro ne kuma baka da 'kwarewa ta musamman a harkar ya'ki (baka saba da ya'ki ba kuma baka san dabarun ya'ki ba), saboda haka ka ja baya. Sai yace: "Kawu baka ji ALLAH yace, Ya ku wad'anda suka yi imani! idan kuka gamu da kafirai kar ku juya musu baya a fagen daga ba? Kana so in shiga wuta?" Muna tsakar yin magana sai aka kawo musu hari wanda yasa muka tarwatse muka rabe muka cigaba da ya'ki. Bayan ya'kin ya tsaya sai aka fara duba gawawwakin wad'anda suka yi shahada. Ina zagayawa ina ganin wad'anda suka yi shahada, wasu jini yana zuba daga jikin su wasu kuma ba'a iya gane su saboda 'kurar da ta turni'ke fuskokin su da jinin da ya rufe fuskokin nasu. Yayin da nake zagayawa sai naga wani a kwance a tsakanin doki jini ya rufe mai fuska yana cewa: Ya ku musulmai ku kira min kawu na Abu Qudama don ALLAH. Da naji sai nayi saurin zuwa gare shi, ban iya gane fuskar shi ba saboda 'kura da jini da tattaka shi da dawakai suka yi. Nace: Gani a kusa da kai. Yace: Ya kai masoyi na! Na rantse da mahaliccin ka'aba mafarki na ya zama gaskiya. Ni ne d'an wannan mai linzamin dokin. Ina jin haka sai na rungume shi, na sumbace shi kuma na goge jinin da yake jikin shi nace: Ya kai abun alfahari na! Kar ka manta da kawun ka Abu Qudama, ka sanya ni a cikin wad'anda zaka ro'ka musu ceto a ranar Qiyama. Yace: Irin ku ba za'a manta dasu ba! Ka goge mun fuska da rigar ka? Riga ta tafi

cancanta, ka bar goge mun saboda ina son gamuwa da ALLAH a wannan yanayin. Wannan matar ta Aljanna (Hur) da na baka labarin ta jiya yanzu haka ina kallon ta tana tsaye tana jira ruhi na ya fita daga gangar jiki na tana cewa: Kayi sauri! Ina kewar ka. Idan ALLAH ya mayar daku gida lafiya ka dau'ki rigar nan taka wacce ka goge jini na da ita ka kaiwa mahaifiya ta kuma kace mata ALLAH ya kar6i kyautar ta". Sai yayi murmushi yace: "Na shaida babu abun bautawa da gaskiya sai ALLAH, bashi da abokin tarayya kuma yana cika al'kawari kuma na shaida Annabi Muhammad bawan ALLAH ne kuma Manzon sa ne kuma ALLAH da Manzon ALLAH masu gaskiya ne akan al'kawarin SU" yana gama fad'in haka sai ruhin shi ya bar jikin shi (ya cika) sai aka bisne shi da kayan jikin shi.

Bayan mun koma Riqqa sai na tafi gidan mahaifiyar wannan yaron nayi sallama da ita, bayan ta fito sai na gan ta cikin damuwa. Tace: "Ka zo ne a matsayin mai rarrashi na (mai taya ni alhini) ko ka zo ne a matsayin mai tayani murna?" Nace: "Ki min bayani, menene rarrashi a gurin ki kuma miye taya ki murna?" Tace: "Idan d'ana ya dawo to lallai ka zo taya ni alhini kenan amma idan kazo sanar min cewa yayi shahada, to tabbas kai mai bushara ne". Nace: "To kiyi farin ciki saboda ALLAH ya kar6i kyautar ki". Tace: "Da gaske ya kar6a?". Nace: "Eh" sai ta d'aga hannu tace: "Godiya ta tabbata ga ALLAH da ya raba ni dashi a duniya (don ya had'a mu a lahira)"

(3)

Mata masu addini basu da yawa a cikin mata masu ilimi. Idan aka ambaci mata masu addini, mutane da yawa suna kawo mata masu ilimin addini ne amma ba haka al'amarin yake ba. Mata masu addini kad'an ne daga cikin masu ilimi saboda ilimi daban aiki dashi daban. Akwai matan da basu da ilimin addini mai yawa amma tare da haka sun fi wad'anda suka tara ilimi addini da amfani da ilimin shiyasa Annabi ya bawa duk wanda yake shirin yin aure shawara akan ya za6i mai addini bai ce mai ilimin addini ba. Mata suna da 'ko'karin neman ilimin addini sama da maza amma wasun su karatu baya musu amfani don basa aiki dashi (ban ce duka ba).

Wani mutum yazo gurin Sufyan bin Uyaina yace: "Ya kai Abu Muhammad! Nazo kawo maka 'karar mata ta ne. Ni ne mafi raini da 'kas'kanci a idon ta" Sufyan bin Uyaina yayi shiru sai kuma yace: "Ta yiwu ka aure ta ne saboda neman d'aukaka? Mutumin yace: "Eh, haka ne Abu Muhammad". Sufyan bin Uyaina yace: "Duk wanda ya auri mace don samun d'aukaka ALLAH zai 'kas'kantar dashi, duk wanda ya auri mace don samun dukiya zai shiga talauci amma duk wanda ya auri mace don addinin ta zai samu duka dau'kaka da dukiya da addini ta hanyar ta". Ya bada labari yace: "Mu hud'u ne maza a gidan mu (Ibrahim da Muhammad da Imran da ni). Muhammad shine babba, Imran shine 'karamin mu, ni kuma ina tsakiyan su. Lokacin da Muhammad ya tashi aure sai ya nemi 'yar dangi ('yar manyan mutane) saboda haka sai ya samu wacce ta fi shi dangi (wacce dangin ta suka fi nashi), Muhammad kuma sai ya nemi mai kud'i saboda haka sai ya auri wacce ta fi shi kud'i

kuma ALLAH ya d'and'ana mishi talauci domin ta talauta shi kuma bata bashi komai ba. Ni sai nayi nazari akan al'amarin su duka. Ma'amar bin Rashid ya ziyarce ni sai na masa magana akan batun kuma na bashi labarin 'yan uwa na sai ya karanto min hadisan Annabi (SAW) guda biyu. Hadisin farko da ya karanto min shine wanda Annabi yake cewa: Ana auren mace ne saboda abubuwa hud'u; Saboda addinin ta ko dangin ta ko dukiyar ta ko kyawun ta. (Sai Annabi yace: amma ina shawartar ka) ka auri mai addini hannun ka zai ribata (zaka ci nasara, ba zaka yi da na sani ba)". Hadisi na biyu kuma shine wanda Annabi (SAW) yace: Mace mafi albarka itace wacce aka bata sadaki mafi 'karanci. Nayi amfani da wad'annan hadisan saboda haka ni da na tashi aure sai na nemi mai addini kuma na bata sadaki mafi 'karanci. ALLAH ya had'a min d'aukaka da arziki da addini duk a sanadiyyar mata ta wacce ta kasance mai addini". Mata da maza wad'anda basu yi aure ba da masu shirin 'karin aure ya kamata a lura sosai wajen za6an akokan rayuwa domin idan aka yi kuskure ana iya shiga damuwar da za'a 'kare rayuwa a cikin ta. Duk wanda yayi aure don kyau ko kud'i ko wani abun duniya zai yi nadama tun kafin aje ko ina. Akwai wani wanda na san ya auri wata wacce ita take son shi saboda kyawun shi amma auren bai je ko ina ba. Ita yarinyar da yake 'yar masu hannu da shuni ce kuma ya 'ki yarda ya aure ta sai suka biyo masa ta bayan gida (ta gurin iyayen shi) suka dinga kashe musu kud'i. Bayan ya aure ta sai suka fara fuskantar matsaloli sakamakon rashin tarbiyyar ta kuma duk abinda ya kawo rainawa take. Bayan sun rabo babbar damuwar shi itace iyayen nata sun kar6i 'ya'yan shi suna gurin su kuma baya so su tashi da irin tarbiyyar gidan su. Wannan duk ya faru ne sakamakon bai auri mai addini ba. Haka kuma yawancin mata masu aure don kud'i ko kyau suna shiga matsaloli sakamakon son zuciyar da suka bi wajen yin aure.

Gudunmawar mata masu addini tana amfanar duniya ne gaba d'aya, idan muka duba rayuwar magabata zamu fahimci haka. Daga cikin magabatan da duniya tafi amfanuwa da rayuwar su da ilimin da ALLAH ya basu akwai imam Malik wanda Manzon ALLAH (SAW) lokacin da yake duniya sai da yayi magana akan imam Malik d'an Anas inda yace: Lokaci ya kusa da mutane zasu dinga dukan hantar ra'kuma (suna zagayawa duniya a kan ra'kuma) don neman ilimi amma ba zasu samu wani mai ilimi ba kamar malamin nan na madina (shine Imam Malik). Shima wannan gwanin namu imam Malik yana cikin wad'anda mahaifiya su ta yi gwagwarmaya wajen karatun shi. Imam Malik yana cewa: "Mahaifiya ta tana shirya ni sai tace min: Ka tafi gurin Rabi'a (Rabi'a bin Abdurrahman kenan kamar yadda muka kawo 'kissar shi da gwagwarmayar da mahaifiyar shi tayi wajen karatun shi) yace da yaje gurin Rabi'a d'in sai ya kuyi ladabin sa kafin ilimin sa".

Wani malami ya ga wani yaro 'karami mai nutsuwa kullum yana zuwa masallaci ana sallah dashi saboda haka sai yaron yana burge shi matu'ka. Malamin nan wata rana ya kira yaron yayi masa wasu tambayoyi yace: "Ka haddace suratul Fil?" Yaron yace: "Eh na haddace". Malamin yace: "Ko ka haddace izu biyar?" Yaron yace: "Eh na haddace". Malamin ya sake tambayar shi yace: "Ko ka haddace izu talatin?" Yaron yace: "Eh na haddace". Malamin yayi mamaki ya 'kara tambayar shi yace: "Ko

ka haddace Qur'ani?" Yaron yace: "Na haddace". Malamin nan ya cika da mamaki kuma ya tambayi yaron nan yace: "Ina ne gidan ku?" Yaron ya yiwa malamin kwatance. Washegari sai wannan malamin yaje gidan su yaron yayi sallama da mahaifin yaron. Da mahaifin yaron ya fito sai malamin ya gan shi bai yi kama da wanda ya bawa wannan yaron ilimi ba. Bayan sun gaisa malamin ya mishi bayani akan yadda yaron ya burge shi wanda hakan ne yasa yaji yana son sanin iyayen shi da salon da suka bi wajen tarbiyyantar da yaron har ya haddace Qur'ani a 'karancin shekarun shi. Mahaifin yaron ya cewa malamin: Wannan aikin mahaifiyar su ne, ta kasance kullum idan ta gama abincin dare za ta fara kar6an haddar su kafin su ci abinci. Duk wanda ya fara bada hadda shi zai fara d'iban abinci kuma duk wanda haddar shi tafi yin kyau shi zai za6i abinda za'a dafa gobe. Da haka ta taimaka musu har suka haddace Qur'ani kuma ba yaron nan kad'ai ba har 'kannen shi akwai wanda ya haddace Qur'ani haka ma yayun shi duka sun haddace".

Akwai wata 'kissa da ta shahara ta wani yaro wanda mahaifiyar shi ta koyar dashi kyakkyawar d'abi'a ta fad'an gaskiya, wata rana yana tafiya cikin ayari sai 'yan fashi suka tare su a hanya kuma suka bu'kaci kowa ya fito da duk kud'in da yake dashi. Sauran mutanen da suke ayarin kowa yace bashi da kud'i amma da aka zo kan yaron nan aka tambaye shi sai yace shi ya taho da kud'i. Shugaban 'yan fashin yace: "Ina kud'in yake?" Yaron yace: "Yana d'aure a cikin kaya". Da aka duba sai aka ga kud'in kuma da aka 'kirga sai aka ga kud'in sun cika dai dai yadda yaron yace. Shugaban 'yan fashin yayi mamaki yace: "Kai kowa yace bashi da kud'i mai yasa kai ka fad'i gaskiya?" Sai yaron yace: "Mahaifiya ta tace kar in ta6a yin 'karya a ko wane yanayi". Shugaban 'yan fashin yayi shiru yana tunani sannan yace: "Idan har mahaifiyar wannan yaron zata koyar dashi ya ri'ke gaskiya a ko wane hali kuma ya fad'i gaskiya har ga wad'anda zasu cutar dashi, to lallai mu yafi cancanta mu koma ga ALLAH muyi gaskiya kuma mu ri'ke gaskiya har 'karshen rayuwar mu". Nan take wad'annan gungun gogaggun 'yan fashin suka tuba daga miyagun ayyukan su duk a sanadiyyar tarbiyyar da mahaifiyar yaron nan ta masa (Abu ne mai muhimmanci iyaye su lura da kasancewar yara basa 'karya sai dai idan an koya musu, idan kuwa iyaye suka tarbiyyantar da 'ya'yan su akan ri'ke gaskiya to fa zasu yi ri'ko da ita tsawon rayuwar su a dukkan al'amuran su kuma su koyar da wasu).

Wata malama tana karantar da yara sai tace kowa ya zana mata dausayi. Wata yarinya sai ta zana Qur'ani, da malamar ta gani sai tace: "Ke kurma ce? Ba dausayi nace a zana min ba?" Sai yarinyar tace: "Ni wannan na iya. Mama na tace min Qur'ani shine babban dausayi". A wani ajin wata makaranta kuma wani malami yana tambayar yaran ajin akan abinda suke son zama idan sun girma sun yi karatu. Kowa yana tashi ya fad'i abinda yake son zama har aka zo kan wani yaro, shi da ya tashi sai yace yana son zama sahabi. Malamin yayi mamaki ya tambaye shi: "Me yasa kake son zama sahabi?" Sai yaron yace: "Mama na kullum kafin in kwanta tana bani tarihin sahabi, tace sahabi yana son ALLAH da Manzon ALLAH shi yasa nake son zama sahabi".

Babu shakka musulunci ya bawa mata daraja da martaba kuma mata masu addini sun taimaki addini da duk damar da suka samu. Mace ce ta fara taimakon addini kuma mata har yau sun fi maza taimakon addini sai dai idan basu samu dama ba. Ko bamu yarda mata sun fi maza taimakon addini ba, dole mu yarda mata sun fi maza tausayi kuma sune silar kwanciyar hankali da rayuwa mai kyau domin ko ba komai yawanci su suke karantar da yara addini kuma tabbas ALLAH yana tausaya mana ne saboda karantar da yara da ake yi kuma shi namiji ko yana da ilimin da zai karantar ba zai iya aikin karantar da yara ba saboda ba zai iya jure reno da hayaniyar su ba, yafi gwammacewa yaje yayi ko da dako ne.

A wannan zamanin mata da yawa sun fi wasu mazan gwagwarmayar neman abinda zasu inganta rayuwar 'ya'yan su dashi. Idan bamu manta ba gwagwarmayar da mata suke saba yi wajen kula da marayun da mazajen su suka mutu suka bar su dasu yasa Annabi (SAW) ya yiwa duk matar da ta tarbiyyantar da 'ya'yan ta ko guda biyu bushara da Aljanna. Fad'i tashin da wasu daga cikin mata suke yi a yau ya kai ga su suke d'aukan nauyin 'ya'yan su wad'anda iyayen su maza suka yi watsi dasu domin maza da yawa sun sakarwa mata nauyin gida. Mata masu addini ko mazajen su suna raye kuma suna sauke nauyin da ALLAH ya d'aura musu na kula da iyalen su, su suke d'aukan nauyin tarbiyyantar da 'ya'yan su da ciyar dasu. Duk abinda mutum ya zama bayan wahalar da mahaifiyar shi tayi a kan shi ne don haka ma ALLAH da Manzon ALLAH suka yi umarni mai 'karfi akan kyautatawa mahaifiya. Wani mutum yazo gurin Abdullahi d'an Abbas yana tambayar sa yace: "Mun yi soyayya da wata mata, daga baya sai na gano ashe taje ta auri wani saboda haka kishi yasa na kashe ta. Shin ALLAH zai yafe min?" Sai Abdullahi d'an Abbas yace: "Mahaifiyar ka tana raye?" Sai mutumin yace: "A'a". Sai Abdullahi d'an Abbas yace: "To kaje ka ta yin ayyukan alkairi kuma kayi ta yin istigfari da tuba zuwa ga ALLAH (mai yiwuwa ALLAH zai yafe maka). Bayan mutumin ya tafi sai wad'anda suke zaune a gurin suka tambayi Abdullahi d'an Abbas suka ce: "Me yasa ka tambayi shi ko mahaifiyar shi tana da rai?" Sai Abdullahi d'an Abbas yace: "Bansan aikin da yake saurin kusantar da mutum zuwa ga ALLAH ba kamar kyautatawa uwa" (Ma'ana duk wanda yake son samun kusanci zuwa ga ALLAH sai yayi 'ko'karin kyautatawa mahaifiyar sa kuma duk wanda yayi babban zunubi kuma yake son komawa ga ALLAH sai ya kyautatawa mahaifiyar shi iyakar kyautatawa). Wahalhalun da iyaye mata suka yi ne silar duk abinda mutum ya zama domin sune sanadin zuwan kowa duniya kuma su ne suka yi renon kowa a duniya duk cikin wahala. Daga haihuwar d'a zuwa girman shi ake mishi tarbiyya kuma a wannan tsakanin ne idan aka yi sa'a mai addini ce ta haife shi kuma ta mai tarbiyya sai shima ya tashi da addini. Yawancin manyan malamai a gurin iyayen su mata suka fara karatu kuma yawancin manyan malamai sun yi karatu a gurin malamai mata (lallai gudunmawar mata masu addini ba zasu lissafu ba). Duk ilimin mutum idan yana so 'ya'yan shi su samu ilimi da tarbiyya dole ne ya za6a musu uwa mai addini.

Duk da hadisi ya tabbata cewa mata ne zasu yawaita a wuta, a fahimta ta har a Aljanna ma mata zasu fi yawa kuma dalilin da yasa zasu yi yawa a wuta shine

yawaitar su a duniya. A duniya mata sun nunnunka maza kuma a aljanna ma zasu nunnunka su. 'Ka'idar shiga Aljanna itace duk wanda yayi aiki mai kyau daga cikin maza ko mata za'a saka mishi da mafi kyawu (wato Aljanna) domin dama an yi tattali da tanadin ta ne don masu imani da aikata mai kyau.

Tarbiyyar mata tafi ta maza wahala kuma tafi riba. Idan ka tarbiyyantar da mace kamar ka tarbiyyantar da duniya ne, idan kuma ka bata ilimi musamman na addini tamkar ka ilimantar da duniya ne.

Mata ne suka haifi wad'anda suka cika duniya da ilimi da albarka haka ma mata ne suka haifi wad'anda suka cika duniya da 6arna da ta'addanci. Yawancin matan da suka haifi wad'anda rayuwar su ta zama haske ga duniya masu addini ne kuma sun tarbiyyantar da 'ya'yan ne, yawancin matan da suka haifi wad'anda rayuwar su ta zama annoba da barazana ga duniya ba masu addini bane kuma basu tarbiyyantar dasu bane.

Matan da suka nemi ilimin addini don ALLAH kuma suke amfani dashi wajen bin ALLAH sune mata masu addini amma duk ilimin mace idan bata nemi ilimin don ALLAH ba kuma bata aiki dashi wajen bin ALLAH, ba mai addini bace. Tarbiyya da ilimi ba wacce zata iya bada su sai tana dasu. Babu sadaka mai gudana mafi riba wacce ko mutum bashi da kud'in gina masallatai da makarantu da sauran su zai iya yi kamar haihuwar 'ya mace da karantar da ita addini. Idan ka haifi mace kuma ka karantar da ita addini to gudunmawar da zata bawa addini bashi da iyaka kuma wanda ya haife ta kuma ya taimaka wajen yin taibiyyar ta da wacce ta tarbiyyantar da ita suna da ladan da ba'a san lokacin da zai tsaya ba. Mahaifi shine jagoran tarbiyya, mahaifiya kuma itace babbar mai gudanar da tarbiyya.

Mahaifiyar nana Maryam 'yar Imran ta kasance mai yawan hidimtawa addini wanda hakan ne yasa tayi bakancen zata sadaukar dashi don ya hidimtawa addini (a zaton ta namiji zata haifa don tana ganin namiji zai fi taimakawa addini sama da mace) sai kuma ALLAH ya bata mace wanda ba haka taso ba amma sai ta saka mata albarka kuma ALLAH ya mata albarka don ta kasance mai addini kuma ALLAH ya fitar da wanda ya zama mafi albarka a zamanin daga tsatson ta. Akwai abun mamaki matu'ka ga wanda baya son haihuwar mace saboda wani ra'ayin nasa kuma akwai wad'anda basa son haihuwar mace ne saboda abinda suka yiwa 'ya'yan wasu don sun san suma za'a yiwa nasu.

Mata masu addini sune jin dad'in duniya kuma sune silar kyautatuwar rayuwar da za ta zo bayan ta duniya, maza suma su zama masu addini saboda sune jagorori kuma su auri mata masu addini domin ayi rayuwa cikin addini kuma a haifi 'ya'ya masu addini da albarka wad'anda zasu taimaki addini da al'umma.